## SŨRATUL KAUTHAR سُورَةُ الكَوثَر

Tana nũna darajar Annabi zuwa ga Allah, yadda Yake yi masa kyauta kuma Ya yi masa faɗa da maƙiyinsa.

بِسْمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحْمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

*Da sũnan Allah, Mai rahama, Mai jin ƙai.*

*1.* Lalle ne Mu, Mun yi maka kyauta mai yawa.

*2.* Saboda haka, ka yi salla dõmin Ubangijinka, kuma ka sõke (baiko, wato sukar raƙumi).

*3.* Lalle mai aibanta ka, shi ne mai yankakkiyar albarka.

إِنَّآ أَعْطَيْنَٰكَ ٱلْكَوْثَرَ ١

فَصَلِّ لِرَبِّكَ وَٱنْحَرْ ٢

إِنَّ شَانِئَكَ هُوَ ٱلْأَبْتَرُ ٣

## SŨRATUL KÃFIRŨN سُورَةُ الكَافِرُون

Tana bayãnin cẽwa ba a sassautawa ga gaskiya game da addini, dõmin nẽman yardar wasu mutãne ko wani mutum.

بِسْمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحْمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

*Da sũnan Allah, Mai rahama, Mai jin ƙai.*

*1.* Ka ce, "Ya kũ kãfirai!

*2.* "Bã zan bautã wa abin da kuke bautã wa ba.

قُلْ يَٰٓأَيُّهَا ٱلْكَٰفِرُونَ ١

لَآ أَعْبُدُ مَا تَعْبُدُونَ ٢

*3.* "Kuma kũ, ba ku zama masu bauta wa abin da nake bautã wa ba.

وَلَآ أَنتُمۡ عَٰبِدُونَ مَآ أَعۡبُدُ ۝٣

*4.* "Kuma nĩ ban zama mai bautã wa abin da kuka bautã wa ba.

وَلَآ أَنَا۠ عَابِدٞ مَّا عَبَدتُّمۡ ۝٤

*5.* "Kuma kũ, ba ku zama mãsu bautã wa abin da nake[1] bautã wa ba.

وَلَآ أَنتُمۡ عَٰبِدُونَ مَآ أَعۡبُدُ ۝٥

*6.* "Addininku na garẽ ku, kuma addinina yanã gare ni."

لَكُمۡ دِينُكُمۡ وَلِيَ دِينِ ۝٦

## SŨRATUN NAṢR سُورَةُ النَّصۡرِ

Tana nũna ƙãrẽwar aikin Annabi na Manzanci, kuma tana nũna abin da tsõho zai kãma yi idan aikin ƙarfi ya buwãye shi.

بِسۡمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحۡمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

*Da sũnan Allah, Mai rahama, Mai jin ƙai.*

*1.* Idan taimakon Allah ya zo da cin nasara.

إِذَا جَآءَ نَصۡرُ ٱللَّهِ وَٱلۡفَتۡحُ ۝١

*2.* Kuma ka ga mutane suna shiga addinin Allah, ƙungiya-ƙungiya.

وَرَأَيۡتَ ٱلنَّاسَ يَدۡخُلُونَ فِي دِينِ ٱللَّهِ أَفۡوَاجٗا ۝٢

*3.* To, ka yi tasbihi game da gõde wa Ubangijinka, kuma ka nẽme Shi gafara, lalle Shi (Ubangijinka) Ya kasance Mai karɓar tũba ne.

فَسَبِّحۡ بِحَمۡدِ رَبِّكَ وَٱسۡتَغۡفِرۡهُۚ إِنَّهُۥ كَانَ تَوَّابَۢا ۝٣

---

(1) Ãya ta 4 da ta 5 sun nũna addinin ƙarya yakan canza amma na gaskiya bã ya canzawa.